MINISTÈRE
DE L'EUROPE
ET DES AFFAIRES
ÉTRANGÈRES
*Liberté
Égalité
Fraternité*

DIRECTION GENERALE DE L'ADMINISTRATION
ET DE LA MODERNISATION

DIRECTION DES RESSOURCES HUMAINES

Sous-direction de la Formation et des Concours

Bureau des Concours et Examens professionnels
RH4B

# CONCOURS EXTERNE ET INTERNE POUR L'ACCÈS A L'EMPLOI DE CONSEILLER DES AFFAIRES ETRANGÈRES (CADRE D'ORIENT) AU TITRE DE L'ANNÉE 2022

---

**ÉPREUVES ÉCRITES D'ADMISSIBILITÉ**

**Mercredi 8 septembre 2021**

# HAOUSSA

Durée totale de l'épreuve : 3 heures
Coefficient : 2
Toute note inférieure à 10 sur 20 est éliminatoire
Barème de notation : composition en haoussa 12 points ; traduction en français 8 points

**TRADUCTION EN FRANÇAIS**

*Traduction en français d'un texte rédigé en haoussa*

TEXTE AU VERSO

**Marasa aikin yi sun ƙaru a Najeriya**

'Yan Najeriya na mayar da martani kan rahoton hukumar ƙididdigar jama'a, da ya nuna cewa yawan marasa aikin yi ya ƙaru zuwa kashi 33.3 cikin ɗari a tarayyar Najeriya.

'Yan Najeriya kaso 33.3 cikin ɗari ne ke fama da rashin aikin yi, wanda wannan shi ne kaso mafi muni na yawan mutane miliyan 23 da ba su da aiki, wanda ya hakan ya ƙara fito da koma bayan tattalin arzikin da Najeriyar ke ciki a yanzu a zahiri.

Ƙaruwar yawan mutanen da ke zaman kashe wando ba don suna so ba bisa yanayin da ƙasa ta samu kanta na ƙara nuna hali na talauci da 'yan Najeriya suka faɗa, duk kasancewarta ɗaya daga ƙasa mafi ƙarfin tattalin arziki a nahiyar Afirka, kuma ta kan gaba da yawan jama'a a nahiyar. Alkaluma nuna cewa 'yan Najeriya milyan 98 ne ke cikin hali na talauci daga adadin mutane miliyan 200 da ƙasar ta ke da su.

Irin halin da Najeriyar ta ke ciki na ƙalubalen rashin tsaro kama daga matsalar ta'adanci zuwa ga rigingimun manoma da makiyaya da masu garkuwa da jama'a, an dade ana danganta su da matsalar rashin aikin yi a tsakanin al'umar ta Najeriyar, kuma masanan Najeriya irinsu Dr Yahuza Getso na ganin cewar hakan ya yi mumunan illa ga rayuwar jama'a, wanda ya ce "Dole ne a tashi haikan don magance matsalar rashin aikin yi ga mutane, da inganta fannin ilimi, idan ana fatan ganin samun sauƙi cikin gagawa."

Bukatar sauyi ga daukacin yanayin da Najeriya ta samu kanta ba zai ta'allaka kawai ga batun rashin ilimi kadai ba, akwai har da rashin ingantaccen ilimin da kwarewar aiki lamarin da ke barazana ga batun tsaro. Tun daga 2016 Najeriya ke samun ƙaruwar marasa aikin yi bisa karayar tattalin arzikinta, wanda ya kuma fannoni da dama cikin matsala da koma baya, duk da yake gwamnatin da ma ta yi hasashen faruwarsa in har ba a ɗauki matakin da ya dace ba.

Uwais Abubakar Idris, Deutsche Welle Hausa 16.03.2021, https://p.dw.com/p/3qhUD